*Kano Journal of Arts and Social Sciences (KAJASS)*
*A publication of School of Secondary Education,*
*Sa'adatu Rimi College of Education Kumbotso, Kano*

# GUDUNMOWAR MASANA WAJEN SAMAR DA AYYUAKAN YI GA AL'UMMA

**Halima Isma'il**
Hausa Department, School of Languiages, Sa'adatu Rimi College of Education Kumbotso, Kano, Nigeria
**Lead Author:** halimaismail1978@gmail.com 08028710969

ISSN: 1119-4596
Submitted at the 3rd National Conference of the School of Secondary Education (Arts and Social Sciences), October 2025. Published as a Special Edition, July 2026

TSAKURE

Masana suna taka muhimmiyar rawa wajen samar da ayyukan yi ga al'umma. Waɗanda suke kawo ci gaba wajen bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa, tare da samar da damammaki na ayyukan yi ga al'umma. Wannan takarda ta ƙunshi nazari a kan rawar da masana suke takawa wajen samar da ayyukan yi ga matasa da ma sauran al'umma gaba ɗaya. Domin ayyukan yi na ɗaya daga cikin ginshiƙan cigaban tattalin arziƙi da zamantakewa ta kowace ƙasa. Haka kuma masana na ba wa al'umma dama ta hanyar gudanar da bincike da ƙirƙire- ƙirƙire da bayar da shawarwari ta fuskoki daban-daban. Haka kuma masana suna taimakawa wajen horar da matasa da samar da dabaru da za su amfana da su ta ɓangarori daban – daban, musamman ayyukan gwamnati da na masu zaman kansu da sana'o'i da kuma kasuwanci da sauran hanyoyi na biyan buƙatu. Wannan takarda ta yi bayani a kan yadda masana suke amfani da ilimi wajen samar da sababbin hanyoyi na bunƙasa sana'o'i da samar da ayyukan yi domin a kawar da rashin aikin yi a tsakanin matasa. Haka kuma takardar ta yi bayani a kan yadda masana suke ilmantar da manazarta da ɗalibai wajen horar da su ilimin da zai ba su damar dogaro da kai. Ire-iren masanan da suke taimakawa wajen samar da ayyukan yi sun haɗa da masana ilimi kamar su malaman Jami'o'i da na sauran makarantu na ilimi mai zurfi da ma na makarantun gaba da sakandare musamman makarantun koyar da sana'o'i, da masana fasaha da ƙere-ƙere kamar su injiniyoyi da masana zane na kowane ɓangare da msana tattalin arziƙi musamman 'yan kasuwa da masana aikin jiya da likitoci da manoma da masana harkokin kuɗi da sauransu.Wannan takarda za ta yi ƙoƙarin cim ma manufofi kamar haka. Fito da wasu muhimman hanyoyi waɗanda za su taimaka wa matasa wajen dogaro da kai. Zaƙulo waɗansu sana'o'i da ayyukan yi waɗanda za su ba wa al'umma aikin yi domin gujewa faɗawa wasu munanan hanyoyi da ɗabi'u marasa kyau. Wajen samo muhimman jawabai na gudanar da wannan aiki. An ziyarci masana ilimi na ɓangarori daban – daban. Haka kuma an samo wasu muhimman bayanai daga malamai da manazarta na jami'o'i da sauran makarantu na ilimi, inda aka shigar a wannan aiki. Muhimmancin da wannan aiki yake da shi, shi ne, domin samo wasu muhimman hanyoyi na samar da sana'o'i ga al'umma da fitar da su daga wani yanayi na talauci domin samar da cigaba da bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa.

**Kalmimon fannu:** Masana, Kirƙire-ƙirƙire,Tattalin arziki ,Bincike, Ilimantarwa, Sana'oi' kasuwanci, Horarwa. Koyo, koyarwa.

## GABATARWA

Masana na taka muhimmiyar rawa wajen gina al'umma, musamman ta ɓangaren samar da ayyukan yi ga matasa domin bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa da samar da aiki yi ga matasa. Ayyukan yi da sana'o'i, na ɗaya daga cikin hikimomi da fasahohi da al'umma kan zaɓa don tafiyar da rayuwarta cikin nishaɗi da jin daɗi domin ɗaukar nauyin kan su da sauran mutanen da ke ƙarƙashin su. Aikin shi ne duk wani aiki da mutum yake yi domin samun wani abu ko samun kuɗin shiga wanda zai taimakawa rayuwarsa. Aikin na iya kasancewa aikin da yake buƙatar ƙarfin jiki, kamar gini da noma da sauransu. Sai kuma aikin da yake buƙatar horo na ilimi kamar likita da malamin makaranta da injiniyoyi da sauransu. Sai kuma nau'in aiki da ba ya buƙatar ƙwarewa ko horo na ilimi kamar masu ɗaukar kaya da masu shara da karan mota da direbobi da sauransu. Duk waɗannan suna daga ayyukan da ake yi domin samun abin masarufi wanda yake taimakawa wajen bunƙasa tattalin arzikin ƙasa. Masana daga ɓangarori daban- daban suna taimakawa al'umma wajen ba su ilimin da koya masu wasu ayyuka da suka danganci ƙirƙire-ƙirƙire da gudanar da bincike a kan wani muhimmin abu na ilimi wanda zai taimaka a gano wani sabon abu da zai taimaka wajen samar da aikin yi da taimaka wa wajen bunƙasa tattalin arzikin ƙasa.Wannan aiki ya ƙunshi fito da muhimman abubuwa da suke taimakawa wajen samar da ayukan yi ga al'umma, waɗanda suke taimaka musa wajen gina rayuwarsa da duk wani da yake tare da su.

## Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce, fito da ire-iren gudummawar da masana na ɓangarori daaban- daban waɗanda suke da ilimi da ƙwarewa da gogewa a wasu fannoni na rayuwa suke bayarwa wajen samar da ayyyukan yi ga al'umma.

Zaƙulo muhimman abubuwa da za su taimaka wajen inganta rayuwar al'umma, tare da bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa

Fito da muhimman hanyoyi na gudanar da sana'a da nuna wa matasa wasu ayyukan yi wanda zai ba su damar dogaro da kai da rage musu talauci da ƙara gina tattalin arzikin ƙasa.

## HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

Kowane bincike yana da muhimman hanyoyi waɗanda ake amfani da su wajen samo bayanai da suka dace da shi Wannan aiki an yi amfani da waɗannan hanyoyi wajen gudanar da shi kamar haka: An samo muhimman bayanai waɗanda suka haɗa da nazartar ayyukan magabata musamman kundayen bincike da littattafai. Haka kuma an tattauna da mutane daban-daban domin ƙara samun haske da ƙarin bayani a kan wannan aiki. Haka kuma an ƙara samun bayanai daga kafafan sadarwa da ake da su domin ƙara inganta aikin da samun madogara na gudanar da aikin.

## GUDUMMAWAR MASANA WAJEN SAMAR DA AYYUKAN YI GA AL'UMMA

Gudummawa shi ne taimako ko goyan baya da wasu mutane ko waɗansu ƙungiyoyi suke bayarwa domin al'umma ta amfana. Gudummawa na nufin taimako na aiki ko kuɗi ko abinci ko sutura ko wani abu. (Kamusun Hausa 2006:171).

Al'umma da dama suna buƙatar gudummawa ta ɓangarori daban-daban, wanda idan aka tallafa musa za a sami al'ummar cikn walwala da jin daɗi domin an ɗauke musu wata damuwa da take tattare da su. Samar wa al'umma ayyukan yi musamman matasa zai taimaka matuƙa wajen rage raɗaɗi da kuma rage zaman rashin aikin yi wanda yakan kai su ga halaka.

**Ayyukan yi**

Ayyukan yi na nufin duk wani ƙwadago na neman halal wanda doka ta tanada wanda mutum ke aikatawa domin ya sami kuɗin shiga ko samin wata fa'ida wajen yi. Aiki shi ne aikace-aikace ko ayyuka. Abin yi ko ƙwadago (Kamusun Hausa 2006:6) Akwai ayyukan ofis da ake yi a matsayin hanyoyin samun kuɗi misalan su, sun haɗa da malami na makarantun ilimi na matakai daban- daban da likitoci da injiniyoyi da ma'aikatan jinya da ma'aikatan gwamnati da masu kamfanoni da ma'aikatan kamfanonin da sauransu da yawa. Sai kuma sana'o'i kamar ɗinki da gini da noma da kafinta da tuƙin mota da gyaran abubuwa irin su mota da gyaran waya da gyaran agoguna da sauransu, Sai kuma kasuwanci, wannan ya shafi saye da sayarwa da yankasuwa masu zama a kasuwa da masu hada – hadar kuɗi ko mamallakan rumfuna da suke ba da haya da sauransu da yawa.

**Ma'anar Koyo**

Kamusun Hausa (2006:250) ya ba da ma'anar koyo da cewa koyo neman sanin abu ta hanyar koyarwar wani, wato malami ko mai ba da horo.

Koyo hanya ce ta sadar da ilimi tsakanin mai koyo da mai koyarwa, domin kawo sauye-sauye na daga abin da aka koya. Koyo na iya samar da wasu muhimman abubuwa na ilimi wanda ya shafi karatu ko rubutu, wanda ke iya kasancewa sabon abu da mai koyo zai iya sarrafa shi da ƙara samun haske a kai.

**Ma'anar Koyarwa**

Koyarwa wata hikima ce ta sanar ko nuna wa mai koyo wani sabon ilimi wanda zai iya zama karatu ko rubutu ko wata hikima (Salihi, 2008: 1)

Kamusun Hausa na Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero Kano ya bayyana ma'anar koyorwa da cewa: Koyarwa na nufin koya darasi ga wani (Kamusun Hausa 2006: 250)

Idan aka yi duba dangane da wannan ma'ana da masana suka kawo, za a iya kallon koyarwa

da cewa : Koyarwa hanya ce ta tarbiyantar da mutum ko ɗalibi darasi domin samun ilimi akan

wani abu na sha'anin rayuwa ya kuma fahimci abin da ake nufi daga ƙarshe a sami mutum

nagartatacce wanda al'umma za ta yi alfahari da shi. Koyarwa hanya ce ta koyar da wani darasi ga ɗalibai domin samar da ingattaccen ilimi.

**Dabarun Koyarwa**

Dabarun koyarwa a kowanne harshe za a iya bayyana su da cewa, duk wata hikima ko salo ko kuma hanya wacce malami koi masani yake ganin amfani da ita zai kawo sauƙi da saurin fahimtar aikin da yake son koyarwa ko nunawa ga ɗalibai ko matasa. Kasancewar koyarwa wata hikima ce ta samar ko nuna wa mai koyo wani sabon ilimi wanda zai iya zama karatu ko kuma rubutu, ko dai wata hikima da kan taimaka wa mai koyo wajen sarrafa wani abu.

**Gudummawar da Masana Suke Bayarwa Wajen Samun Ayyukan yi**

Masana na nufin mai ilimi ko gwani ko masanin faruwar wani abu.(Kamusun Hausa 2006:335)

Masana su ne mutanen da suke da ilimi da ƙwarewa da gogewa a wani fanni na rayuwa. Kamar ilimi na fannin fasaha, ilimn lafiya, ilimin noma, da masana'antu da sauransu. Haka kuma waɗannan masana, suna amfani da limi wajen warware matsaloli ko amfani da su wajen samar da cigaba a cikin al'umma. Ire-iren masana da ake da su sun haɗa da: Malaman jami'o'i (Lecturers) da masu gudanar da bincike (Researchers) da masana ilimin fasaha (Engineers) da masana ilimin tattalin arziki da likitoci da masana sana'o'i da masana magunguna (Pharmacists) da masu koyar da ayyukan yi da suka danganci

sana'a (Entrepreneurs) Waɗannan masana su ne waɗanda suke da ƙwarewa suke da ilimi suke kuma amfanar da jama'a ta ɓangarori daban- daban.

**Masana Ilimi Musamman Malamai na Jami'a da Sauran Makarantu**

Masana ilimi, musamman malamai suna ba da muhimmiyar gudummawa wajen samar da ayyukan yi, sukan horar da matasa da ilimin da zai ba su damar samun aiki ko ƙirƙirar sana'a, a kan duk wani abu da mutum zai yi ya samu abubuwan masarufi ya kuma rufawa kansa asiri .Waɗannan masana suna ba da shawarwari a kan yadda za a ɓullowa da wasu matsaloli da hanoyin samun mafita.. Haka kuma suna horar da al'umma musamman matasa wajen koya musu ilimi na neman sana'a. Misali Malaman da suke koyar da harshen Hausa suna samun ayyukan yi ta amfani da harshen Hausa. Sukan fassara abubuwa daga Turanci zuwa Hausa, ana ba su gyararraki na wasu abubuwa domin a sami daidaitacciyar Hausa. Haka kuma suna samun ayyuykan yi a gidajen rediyo da talabijin, ana kuma ba su matsayi na karanta labarai da harshen Hausa. Haka kuma sukan fassara littattafai daga harshen Turanci ko harshen Larabci zuwa harshen Hausa.Wannan ma ya taimaka musu wajen ƙara samun ayyukan yi da ƙara bunƙasa tattalin arzikin ƙasa. Haka kuma Malaman Turanci sukan yi duk ire-iren abubuwan da Malaman Hausa suke yi, amma ta fuskar turanci. Malaman Arabiya ma ba a bar su a baya ba domin suna gudanar da nasu abubuwan da Larabci. Haka kuma duk sauran harsuna da ake da su, suna gudanarwa da harshensu, duk domin samun abin masarufi da samun rufin asiri tare da bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa.

**Masana Fasaha da Kere-Kere**

Waɗannan masana sun haɗa da injiniyoyi da, ma'aikatan Komfuta (computer) da masu ƙirƙira, da sauransu. Masana suna taimakawa wajen samar wa al'umma ayyukan yi. Sukan ƙirƙiri sababbin hanyoyi na gudanar da wasu ayyuka na fasaha da na'urori da ake buƙatar ma'aikata domin tallafawa matasa samun abin yi da tsallakar da su daga zaman banza. Haka kum a suna kafa kamfanoni da cibiyoyi na horo domin tallafawa matasa.

**Masana Aikin Noma**

Waɗannan masana suna inganta hanyoyin noma da kiwo wanda yake samar da damammakin aiki a cikin bunni har ma a ƙauyuka. Haka kuma ana taimakawa manona da dabarun noma na zamani domin samun ingantattun kayan masarufi. Masana na wannan ɓangare suna taimakawa wajen samar da ayyukan yi da inganta rayuwar al'umma.

**Masana Shari'a da Shugabanci**

Waɗannan masana suna taimakawa wajen samar da ayukan yi, waɗannan masana suna tsara dokoki da manufofi waɗanda suke taimakawa da goyon bayan ƙananan sana'o'i da kamfanoni. Haka kuma suna faɗakarwa a kan yadda ake gudanar da sana'o'i. Suna kuma karɓar ƙararraki da suka danganci matsalolin da masu gudanar da sana'o'in suke fuskanta.

A taƙaice dai kowane fanni na masana yana da rawar da yake takawa wajen inganta rayuwar al'umma ta hanyar samar da ayyukan yi kai tsaye ko a kaikaice.

**Gudummawar da Masana Suke Bayarwa Wajen Gina Tattalin Arziƙi**

Gudummawa na nufin taimako na aiki ko kuɗi ko abinci ko sutura ko wani abu. (Kamusun Hausa 2006:171). Gudummawa taimako ne ko goyan baya da wasu mutane ko waɗansu ƙungiyoyi suke bayarwa domin al'umma ta amfana. Misali Malamai na ba da gudummawa ta ɓangaren koyarwa suna kuma ba da shawarwari a kan karatu ko duk wani abu da ya danganci koyarwa. Haka kuma

likitoci na ba da gudummawa, gudummawar likitoci ita ce kula da lafiyar marasa lafiya, da horar da ɗalibai masu koyan aikin likitoci. Sannan suna ba da shawarwari a kan yadda za a ɓullowa wasu cututtuka da suke addabar al'umma da yanayin yadda za a kula da waɗannan cututtuka, a samar da maganinta.

Masana suna taka mihimmiyar rawa wajen bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa. Haka kuma suna ba da taimako iri daban -daban wajen cigaban al'umma da samar da ayyukan yi. Misali suna taimakawa wajen ilimantarwa da horarrwa da gudanar da bincike da bayar da shawarwari da ƙirƙire-ƙirƙire na sababbin abubuwa da koyar da kasuwanci da sana'o'i da faɗakarwa da koyar da tattali da haɗin gwiwa da sauransu.

## Ilimantarwa da Horarwa

Ilimi shi ne sani musamman na sharia da addini da Karatu na fannin kimiyya da adabi. Ilimi shi ne ganewa ko fahinta. (Kamusun Hausa 2006:205) Ilimantarwa shi ne horarwa a kan wani abu ko karatu ko wani aikin. Horarwa shi ne koyawa ko ladabtarwa. Hora na nufin ladabtarwa da koyawa. (Kamusun Hausa 2006:201)

A wannan ɓangare masana suna taka mihimmiyar rawa wajen ilimantar da al'umma tare da ba su horo a kan wani aiki ko wata sana'a. Suna ba su horo a kan waɗansu sababbin dabaru na ilimi ko na wasu sana'o'i da zai ba su damar dogaro da kai.

## Bincike da Shawarwari

Masana suna ba da gudummawa wajen koyawa ɗalibai da sauran matasa yadda za a gudanar da bincike a kan wani abu domin gano hanyoyi na magance wasu matsaloli da samar da bayanai a kan a bin da ake nema. Haka kuma suna taimakawa wajen ba da shawarwari musamman yadda za a yi maganin ko za a kau da rashin aikin yi ga al'umma.

## Ƙirƙire –Ƙirƙire

Ƙirƙira shi ne ƙagowa ko gano hanyar yi ko samar da wani abu. Ƙirƙira shi ne ƙago ko gano hanyar yi ko samar da wani abu.(Kamusun Hausa 2006:282)

Masana suna taimakawa wajen samar da sababbin fasahohi da ƙirƙire-ƙirƙire da suke buɗe sababbin sana'o'i da ayyukan yi da sababbin masana'antu. Al'umma na samun abin yi ta ƙirƙire- ƙirƙire. Waɗanda suke taimakawa wajen bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa. Haka kuma suna taimakawa matasa wajen samun abin yi da biya wa kansu buƙatu na yau da kullum, da ma ɗaukan nauyin waɗansu daga cikin 'yan'uwa.

## Kasuwanci da Sana'o'i

Kasuwanci na nufin sana'ar saye da sayarwa a kasuwa. (Kamusun Hausa 2006: 238) Sana'a na nufin aikin da mutum yake yi don samun abinci. Misali noma da wanzanci da gini da aski da sauransu. (Kamusun Hausa 2006: 387)

Masana suna taka muhimmiyar rawa wajen taimakawa al'umma musamman matasa wajen ba su sana'ar yi. Sukan gina wasu masana'antu ko kuma kamfanoni su ɗauki ma'aikata aiki su kuma riƙa ba da horo a masana'antun. Wannan wata babbar gudummawa ce wacce take taimakawa wajen ƙara bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa da taimaka wa al'umma wajen samun ayyukan yi domin ɗaukar ɗawainiyar kansu da ma duk waɗanda suke a ƙarƙashinsu.

## Tallafi da Haɗin Guiwa

Dangane da tallafi da haɗin guiwa kuwa masana na ɓangarori daban- daban suna samar wa matasa abubuwan yi, musamman yadda suke haɗa kai da wasu ƙungiyoyi da gwamnati wajen shirya ayyuka da horarwa ga matasa domin su sami abubuwan yi su ragewa kansu zaman kashe wando.Wannan taimako da akan yi wa matasa yana taimaka

musu tare da inganta rayuwar al'umma musamman matasa marasa aikin yi. Haka kuma, samar musu da wannan aiki yana kawo musu mafuta tare da bunƙasa tattalin arziƙin ƙasa.

### Faɗakarwa da Wayar da Kai

Masana na kowane ɓangare suna ba da gudummawa wajen faɗakarwa da wayar da kan al'umma musamman matasa wajen samun aikin yi. Haka kuma ana wayar musu da kai da nuna musu muhiummancin ilimi da muhummancin aiki da ma sana'a. Malami yakan ba wa ɗalibansa shawara tun yana karatu domin ya san abin da ya dace da shi idan ya kammala karatunsa. Haka kuma ta kafafan watsa labarai irin su, rediyo da talabijin da wayar tafi da gidanka da tarurruka ana wayar da kai kan muhimmancin ilimi da aiki da sana'a.

### SHAWARWARI

Shawarwari a kan samar da ayyukan yi ga al'umma da za su taiumaka wajen gina rayuwarsu musamman matasa. Wannan aiki yana mai ba da shawara a kan inganta ilimin zamani da horar da matasa kan sana'o'i daban-daban da fasahar zamani da horar da su a kan kasuwanci da horar da su kan waɗansu sana'o'i musamman sana'o'in da suka shafi gyaran kayayyaki da sauransu. Wannan aiki na daɗa ba da shawara a kan Gwamnati da sauran ƙungiyoyi da manyan 'yan kasuwa da masu hannu da shuni da su tallafa wa matasa domin samun jari na gudanar da sana'a. Haka kuma a tallafawa 'yan kasuwa masu ƙarancin jari da masu ƙananan sana'o'i da rance ko kayan aiki ko ma kyauta da abin da ba zai gagara ba domin su faɗaɗa kasuwancinsu, su kuma yi amfani da wannan dama, su ɗauki ma'aikata aiki. Ɗaukar ma'aikatan zai samar wa da wasu matasan aikin yi.
Haka kuma ana ba da shawara da a kafa cibiyoyin sana'o'i a kowane yanki domin a bawa matasa dama ta samun abin yi.
Ana ba da shawara da a ƙarfafa aikin noma a kuma bunƙasa noman musamman na zamani , a inganta noman da kayan aiki da horror da manoman da tallafa musu, a mayar da noma wata babbar hanya ta samun aikin yi ga matasa. Wanda zai sa a ɗauki matasan aiki, aikin ya zama ko da yaushe, ba sai shekara-shekara ba.
Ana ba da shawara da cewa , gwamnati da masu hannu da shuni da sauran masu zaman kansu da su taimaka su zuba jari a sababbin fasahohi da ake da su domin samar da sababbin ayyuka domin
Tallafa wa matasa wajen samar musu da aikin yin.
Haka kuma ana ba da shawara da a rage dogaro da aikin gwamnati, a wayar wa da matasa kai da muhimmancin dogaro da kai ta fuskar kasuwanci ko sana'o'i.
Ƙarfafa haɗin guiwa tsakanin gwamnati da masu zaman kansu. Yana da kyau a haɗa kai a tsakanin su domin samar da abubuwan yi da rage zaman banza da ƙarancin ayyukan yi. Waɗannan shawarwari za su taimaka wajen rage rashin aikin yi da talauci da ƙarancin kuɗin shiga a cikin al'umma.

### SAKAMAKON BINCIKE

Wannan aiki ya gano cewa masana na taka muhimmiyar rawa wajen samar da ayyukan yi ga al'umma ta fannoni daban- daban. Wannan bincike ya gano abubuwa kamar haka:
Binciken ya gano cewa masana na taimakawa wajen koyar da sababbin dabaru da fasahohi ga matasa, ta wannan hanya ce suke samun damar samun aikin yi ko ƙiƙƙirar sana'o'insu na kansu.
Haka kuma aikin ya gano cewa masana suna gudanar da bincike da ƙirƙire ƙirƙire da ke haifar da sababbin hanyoyin samun aiki. Musamman a fannonin fasaha da noma da ilimi.
Haka kuma an gano cewa masanan na taka rawa wajen ba da shawarwari da tsara manufofi. Inda Gwammati take anfani da

shawarwarin da manufofin da ra'ayoyin wajen inganta tsare-tsaren na samar da aikin yi.
Aikin ya sake gano cewa wasu masana sukan kafa kamfanoni ko cibiyoyi da suke ɗaukar matasa aiki kai tsaye.
Aikin ya gano cewa haɗin guiwar masana da hukumomi na da matuƙar tasiri wajen rage zaman banza na rashin aikin yi da bunƙasa tattalin arziki.
Haka kuma an gano cewa masana na amfani da kafafan sadarwa don wayar da kan al'umma kan muhimmancin sana'a da ilimi da kuma dogaro da kai.

## KAMMALAWA

Masana suna taka muhimmiyar rawa wajen gina al'umma, musamman ta koya musu wasu muhimman abubuwa da za su dogra da kansu. Gudummawar da masanan suke bayarwa suna da matuƙar tasiri ga al'umma musamman matasa, wajen samar musu da ayyukan yi. Masana na kowane ɓangare suna taka muhimmiyar rawa wajen samar da ayyukan yi ga al'umma musamman matasa masu tasowa, domin a rage zaman banza da kau da rashin aikin yi.Wannan takarda ta yi duba a kan yadda masana na ɓangarori daban- daban suke taimakawa wajen samar wa da matasa da ma al'umma baki ɗaya ayyukan yi. Inda aka kawo ire-iren ayyukan da hanyoyin gudanar da su, da kuma yadda za a tallafa wa matasan domin dogaro da kai. Haka kuma da yadda za a kawar da rashin aikin yi a tsakanin matasa. Haka kuma da yadda za a wayar wa da matasa kai da ƙarfafa musau guiwa domin ci gabansu da ma ƙasa gaba ɗaya. Sannan daga ƙarshen takardar an kawo shawarwari da sakamakon bincike, sai aka ƙarƙare da manazarta.

## MANAZARTA


Carlson, S. & Gadio, C.T.( 2002) Teacher Professional Deɓelopment in the use of technology" in Haddad, W. D & Draɗler, A Technology for Education: Potential, parameters and prospects, UNESCO and the Academy for Educational Deɓelopment Paris.

CNHN (2006) *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Leech, G. & Candilin, C.N. (Eds.) (1986). Computers in English Language Teaching and Research, Harlow: Longman.

Mahe, I,A, da Mukhtar, S.M (2013)'Koyarwa da Harshen Hausa: Hanya Mafi Dacewa Wajen Bunƙasa Ilimi a Nijeriya. The Writer, Ɓol.3. Journal of Language, Literature and Teaching Methodology; School of Languages, Sa'adatu Rimi College of Education Kumbotso, Kano.

Mamud, I. da Mudassir M.H (2000) hanyar koyarwa: kundin nazari da aiki sashen koyar da Hausa, kwalejin ilimi ta Sa'adatu Rimi Kano.

Salihi, T. M. (2008) Waiwaye a Kan AIkin Koyarwa Bugu na Uku, Kano Typeset and Published TS Computer Serɓice.

Zarruk, R.M (1979) "Siffofin aikin koyarwa, Ibadan: oɗford uniɓersity press Ltd.